# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tsabta
## Kashi na biyu: Gasasshiyar ayaba mai toka


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Nkoji C. Muhoho |
| Wanda ya tace: | Maja Braun |
| Wanda ya fassara: | Kabir Isa Jikamshi |


**'Yan wasa:**

| | |
|---|---|
| Bilkisu: | 'yar shekara 40 |
| Mariya: | 'yar shekara 43 |
| Hadiza: | 'yar shekara 15 |
| Sama'ila: | ɗan shekara 17 |
| Adamu: | ɗan shekara 36 |

**MAI GABATARWA:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin shirinmu na na “Ji Ka Karu” wanda yake ba da ƙarin haske game da tarin matsalolin da ke tattare da cutar gudawa. A wasanmu na farko mun fahimci cewar Sama’ila ya kamu da cutar gudawa, inda har ma mahaifiyarsa Bilkisu ta ce za ta nemi shawarwari daga surukinta Adamu da matarsa Dokta Husaina waɗanda dukansu ma’aikatan kiwon lafiya ne. Shin ko jinjira Fati za ta yi nisan kwana? Sai a kasance da mu domin jin yadda shirin yake.

**Fitowa ta 1: A gidan Bilkisu**

Mariya, Bilkisu, Hadiza

**BILKISU** Shigo! Kofar a buɗe take.

**MARIYA** Ina kwana, Bilkisu? A’a! Kada ki faɗa min cewa har yanzu jinjirarki tana ci gaba da kukan nan domin tun kafin in shigo nake jin muryarta.

**BILKISU** Ina kwana, Mariya? Ki gafarce ni. A irin waɗannan lokutan ne nake matuƙar begen mijina da ya rasu. Da zai san abin da zai yi game da ciwon da ke addabar yaran nan.

**MARIYA** Allah ya ji ƙan Baban Sama’ila! Kuma ina ci gaba da la’antar direban da ya kashe shi a hatsari. Amma tun da ba ya nan, Allah ya sa ya huta, yayin da ke da ni kuma, ya zama wajibi mu samo maganin cutar da ke addabar Fati a ciki. Na zo da ’yata Hadiza domin ta taimaka mana.

**HADIZA** Yaushe Uncle Adamu da Anti Husaina za su?

**MARIYA** Hadiza, zo nan, ki kunna waccan wutar, yayin da ni kuma zan fere wannan ɗanyar ayabar. Ga alama jinjira Fati tana barci, kin ga ya zuwa lokacin da za ta tashi, ayabar ta haɗu.

**MAI BA DA LABARI:**

Ayaba da wuta? Ga dukan alamu Mariya ta sake takalo wani abin. Ko ta san cewa kuwa tana ƙoƙarin yin maganin ɗaya daga cikin cututtukan da suka fi yin kisa a Afirka ne?

**Fitowa ta 2: A gidan Bilkisu**

Mariya, Bilkisu, Hadiza

| | |
|---|---|
| **MARIYA** | Bilkisu, ƙawata. Bari in yi miki bayani game da wannan sinadari na maganin ruɗewar ciki. Wannan ya fi maganin zamani inganci. Hadiza, ki tabbatar akwai toka mai yawa a wutar. |
| **BILKISU** | Toka? |
| **MARIYA** | E, toka mai zafi. Yanzu, ki fere wannan tsanwar ayabar. Ku turbuɗe ta, ku ɗumama su a cikin tokar, ku rufe su ruf, dole su dahu a cikin tokar. |
| **HADIZA** | Amma suna da tauri. Kuma ta yaya za mu iya fitar da tokar daga jikin ayabar? |
| **MARIYA** | Wane ne ya yi batun cire tokar daga jikin ayabar? Kuma wane ne yake son ayaba mai taushi bayan ciki ya tsure? Maganin zai fi inganci idan ayabar tana da tauri da kuma toka mai yawa a jikinta. |
| **BILKISU** | Ta yaya hakan zai yi amfani, Mariya? Yanzu fa, kin sa ni cikin damuwa. |
| **HADIZA** | Ina ga ya kamata mu tafi asibiti yanzu. Ya zama wajibi mu tafi! |
| **BILKISU** | Hadiza, kada ki damu. Adamu zai iso nan ba da daɗewa ba, kuma zai faɗa mana abin da za mu yi. A ko da yaushe, yana |

da masaniya game da abin da za a yi kan batutuwan kula da lafiya.

**HADIZA** Adamu zai zo yau? O, Alhamdulillah, ya yi kyau!

**MARIYA** Wai shin ku biyun nan, mene ne ba ku fahimta ba? Jinjira Fati tana buƙatar ta ci ayabar da aka lulluɓe ta da toka. Wannan ayabar mai tauri da tokar da aka haɗa ta, za su ɗaure mata ciki da kuma 'yan hanjinta. Wannan zai sa cikin-cikin ya yi tauri, hakan ya sa gudawar ta tsaya, domin a kawo ƙarshen gudawar da ta addabi gidan nan. Mene ne daga cikin waɗannan ba ku gane ba?

**HADIZA** Yanzu kam na shiga cikin damuwa. Don Allah, kana ina Adamu? Don Allah ka zo da sauri! … Ina Sama'ila?

**BILKISU** Yana cikin ɗakinsa. Jikinsa ya yi liƙis, ba ya da ƙarfi. A 'yan kwanakin nan yana yin barci mai yawa.

**HADIZA** Bari in je in gan shi.

**MARIYA** Kul! Kul, Hadiza. Budurwar arziki ba ta zuwa ɗakin saurayi. … Ina jin na makaro. Anya kuwa yaran zamani suna sauraren abin da muke gaya musu? A'a! Kai!

## Fitowa ta 3: A ɗakin Sama'ila

Hadiza, Sama'ila, Mariya

**HADIZA** Sama'ila, Sama'ila! Ka tashi? Yaya jikin?

**SAMA'ILA** Wash! Ina lafiya, amma jikina ba ƙarfi.

**HADIZA** Assha! Ka ga yadda jikinka ya lalace kuwa?

**SAMA'ILA** Na gani, Hadiza, na gode. Yanzu kam ina jin dama-dama.

**HADIZA** Sama'ila, ka gafarce ni. Ba wai ina son ɓata maka rai ba ne. Ka yi haƙuri, na san ba ka da lafiya. Ko zan iya… ko zan iya karanta maka wani littafi?

**SAMA'ILA** Hakan zai yi kyau, amma ɗan zauna nan kawai mu yi hira.

**HADIZA** Zan iya rera waƙa?

**SAMA'ILA** Ke? Waƙa? Ba za ki iya yin waƙa ba!

**HADIZA** E? Zan iya! Kuma mai daɗi.

**SAMA'ILA** Hadiza ke nan. Za ki iya yi mini irin waƙar nan mai sanyaya zuciya? Da hakan ya yi kyau! Ina kika samo wannan waƙa?

**HADIZA** Waƙa ce da za ta taimaka maka. Ni na ƙirƙiro ta domin kai! Za ta taimaka maka ka yaƙi cutar gudawa.

**SAMA'ILA** Waƙar soyayya ce?

**HADIZA** Sakarai! Wata waƙa ce wadda za ta kori cutar. Ka ji yadda take:

*Ka wanke hannuwanka,*
*ka wanke hannuwanka,*
*ka wanke hannuwanka*
*a yayin cin abinci.*
*Malallatan mutane*
*ba sa wanke hannu*
*a yayin cin abinci*
*da bayan sun fito*
*daga banɗaki a kullum.*

Ka ji yadda take.

**MARIYA** Hadiza! Hadiza, ki fito daga ɗakin nan yanzu-yanzun nan! Ɗakin Sama'ila ba wurin ɗaukar waƙe-waƙe ba ne cikin faifai! Akwai aikin da za ki yi. Maza maza ki fito kafin in ƙirga uku! Ɗaya ... biyu …

**MAI BA DA LABARI:**

Kun ji fa, anya kuwa mahaifiyar Hadiza ta yi murna da wannan waƙa mai kyau da 'yarta ta rera? Abin da ya fi muhimmanci dai ga Hadiza shi ne, ta ga murmushi ko yaƙe daga fuskar Sama'ila. A ɗaya gefen kuma, ayaba ta kamala gasuwa a cikin wuta.

**Fitowa ta 4: A gidan Bilkisu**

Mariya, Bilkisu, Hadiza, Adamu

| | |
|---|---|
| **MARIYA** | Bilkisu, babu shakka jaririyar nan taki tana da ƙarfin zuciya. Bari ki gani, idan ta ci ayabar nan za ta yi shiru kamar wata mai ƙoshin lafiya. |
| **BILKISU** | Ya iso! Wancan motar Adamu ce. |
| **HADIZA** | Ai kuwa shi ne. Shi ne! Uncle Adamu ya zo! |
| **ADAMU** | Sannunku dai! A'a! Me ya sa jaririyar nan take kuka ne? Kai! Warin me nake ji ne haka? |
| **HADIZA** | Uncle Adamu, Fati ba ta da lafiya, tana fama da gudawa. Na faɗa musu, sun ƙi su kai ta asibiti. Kuma ga shi ƙafafun Sama'ila ba ya iya yin gudu saboda cikinshi ya tsure da gudawa. Yanzu haka yana kwance, yayin da ake dafa ayaba. |
| **ADAMU** | Me ne? |
| **BILKISU** | Adamu, surukina. A gaskiya ka kyauta da ka zo ganinmu. |
| **MARIYA** | A'a, Malam Adamu ne, ashe ka iso. |
| **ADAMU** | Na yi farin cikin ganinki, Mariya. A'a! Bilkisu, me yake samun Fati take ƙwale kuka haka? Bari in duba ta. … Assha! A'a'a'a! Wannan yarinyar tana fama da rashin lafiya sosai. Bilkisu, ya kamata a ce wannan yarinya tana asibiti. Dubi yadda fatar jikinta ta bushe, ta zubar da ruwa mai yawa, jikinta yana da ƙarancin ruwa. Na ga kuma ta ƙara zama 'yar matsitsiya. |

| | |
|---|---|
| | Duba, yaushe ne ma na gan ta? Watanni biyu ne da suka wuce. Ta daina girma ne? Ko mene ne yake faruwa? |
| **MARIYA** | Bari in gaya maka Adamu, ba na buƙatar irin iliminka kafin in san cewa ƙwayayen halittar jinjira Fati irin na iyayenta ne. “Ta daina girma”, ka ji maganar banza. Kalli Bilkisu, ita gajeruwa ce. Shi kuwa Baban Sama'ila, Allah ya ji ƙansa, ba shi da alamun yin tsawo. Idan haka ne, a wane dalili ne Fati za ta yi tsawo? Kai Malam, magana ce ta gado kawai. |
| **HADIZA** | Tana da cutar gudawa, Uncle Adamu. Na sha faɗa musu. |
| **MARIYA** | Ki rufe mana baki, 'yammata! |
| **ADAMU** | Tun yaushe take gudawar? |
| **HADIZA** | Kwanaki masu yawa, amma sai aka riƙa dafa ayaba da toka… |
| **MARIYA** | 'Yammata, na ce ki rufe mana baki! |
| **ADAMU** | Ayaba? Mene ne alaƙar ayaba da wannan rashin lafiya mai tsanani? Yanzu za mu kai ta asibiti, yanzu-yanzun nan. Mu tafi! Kaico! Allah ya sa dai mu dace. Ina fata dai ba mu makara ba. |
| **BILKISU** | Haba, aaah! Me na yi wa 'yata? |
| **ADAMU** | Cutar gudawa tana da hatsari sosai. Za ta iya yin kisa. Ya kamata a kai Fati asibiti cikin kwanaki bakwai da ta fara gudawa. Wasu 'yan sa'o'i kaɗai na cutar gudawa za su iya sanya yaro ya yanƙwane sosai-sosai, saboda ruwan da ya yi asara a jikinsa, kuma… kuma… ba dai na son furta. A dai bar maganar, ya kamata Bilkisu ta shiga motata yanzun nan. |
| **HADIZA** | Uncle Adamu, don Allah zan bi ka mu tafi tare. |
| **MARIYA** | To kuma, wane ne zai ci ayaba da na sanya wa toka? |

**MAI GABATARWA:**

Halin da jinjira Fati ke ciki ya yi tsanani, an danne hannu kafin a tafi wurin likita domin maganin cutar gudawa da take fama da ita. Kamar wasu yaran Afirka masu yawa ita ma Fati tana fuskantar mugun hatsari wanda zai iya sa cutar gudawa ta yi sanadiyyar mutuwarta saboda jahilci.

Sai a shiri na gaba, inda za ku ji yadda mutanen gidan su Sama'ila ke ci gaba da yaƙi da cutar gudawa. Kuna iya ziyartar shafinmu na yanar gizo domin sake sauraron wannan shiri, wato www.dw-world.de/lbe.